Zagin musulmi fasiƙanci ne, kuma yaƙarsa kafirci ne

Daga Abdullahi ɗan Mas’ud - Allah Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Zagin musulmi fasiƙanci ne, kuma yaƙarsa kafirci ne".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya hana musulmi ya zagi ɗan uwansa musulmi, kuma hakan yana daga fasiƙanci shi ne fita daga yi wa Allah ɗa'a da ManzonSa - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, kuma yaƙar musulmi ga ɗan uwansa musulmi yana daga ayyukan kafirci, sai dai hakan kafirci ne ƙarami.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5333